Cairo Univ. Stud. Rev. Vol. ( 39 ) ( 2016 ) : 55 - 66

# ZANE A MATSAYIN AL'ADAR GARGAJIYA TA MATAN HAUSAWA.

*By*

**NASARA BELLO DOGON DAJI**(*)

**Abstract :**

Design is the creation of plan or convention for construction of an object, or a system as an architectural blueprint. It is a visual communication in form of design. Traditional designers use various methods like creating words, symbols, images, graphs to create a visual representation. A designer may use a combination of typography, visual arts to produce a final result. Hausa women just like their counterparts in other part of the world acquire this skill of design as one of the peculiar craft of women in Hausa society. One of the importants of this design as discovers by this paper is it helps to create cultural identities of the society. This paper attempts to explore these identities as a precursor of Hausa traditional design, adopted by Hausa women as a skill to earn a living.

(*) DEPARTMENT OF NIGERIAN LANGUAGES, SOKOTO STATE UNIVERSITY, SOKOTO, NIGERIA.

## 1.0 Gabatarwa

Zane hanya ce ta ƙawatar da abu domin ya zama abin sha'awa ga idon mai kallo. Wasu lokuta kuma yakan kasance ɗauke da wani saƙo na kalmomi ko surori. Wannan basira akwai ta a cikin al'ummomi daban-daban, sai dai kowace al'umma da irin nata. Allah (SWT) ya halicci ɗan adam da son abu mai sha'awa da ɗaukar hankali, wannan ya sanya duniyarmu a yau ta koma ta zane. Ta hanyar zane ake zana yanayin gida da mota da tufafin sanyawa da kayan ƙawa da kayan aiki da abubuwa masu farantawa da sanyaya zuciya da manyan birane baki ɗaya. Kenan muna iya cewa zane yana da tasiri ga zamani, kuma yana jagorantar al'amurran rayuwarmu ta yau da kullum.

Hausawa suna da hanyoyinsu na gargajiya da suke yin zane ta ɓangarori daban-daban. Akwai zanen da ya shafi gine-gine, wanda ake ƙawata gini, musamman gine-ginen sarauta. Wasu lokuta ma har ga gini na talakawa ma ba a bar shi hakan ba, domin kuwa bayan an yi daɓen gini, ana sa yatsun hannun a yi zanen layi-layi ko kara-kara. Wannan yana nuni ga alama ta al'adar tantance al'ummar Hausawa.

### 1.1 Rabe-raben zane

Akwai rukunin nau'in da ya shafi jiki da al'ummomi ke yi, wanda mafi yawan Hausawa suna yin nasu ne a fuska domin tantance asali da ƙabila, wanda aka fi sani da tsage-tsagen gargajiya (gado). Wannan zanen na fuska da aka fi sani da tsaga yana taka muhimmiyar rawa wajen fito da bayanai da suka shafi asalin mai tsagen, domin da shi ake bambancewa tsakanin Bagobiri da Bazazzagi ko Bakane da Bakatsine sauransu. Sai kuma tsagen da ake na ado, wanda ake yin tsagen jiki na takutaha da ƙayar kifi da shatane da kalangu da 'yar baki da ƙadangarwa da ake yi wanda mafi yawa 'yan mata aka fi sani da shi. Ana kuma yin tsage na waraka daga cuta, kamar ƙaho da kuma tsagar targade da sauransu. Rukunin zane na biyu shi ne nau'in zanen kayayyaki da suka haɗa da zanen maƙera da suke yin ƙota da wuƙa da takobi da adda su ake kira maƙeran baƙi. Akwai kuma maƙeran fari da su ke ƙera kayan ƙawa kamar sarƙa da munduwa da zobe da kujerar ƙarfe da tsinke da sauransu. Sai wasu kayan sana'o'in gargajiya da su ma ana zane su da suka shafi kayan itace da duma. Rukuni na uku ya haɗa zanen wurare da ake na zanen gida da na ɗaki da itace da tsaunuka.

Daga cikin nau'in kayayyakin sana'o'in gargajiya na aiki da ake yin zane gare su, zanen ya kasu gida biyu. Akwai zanen aska wanda maza suka fi yi na kayan aiki musamman ƙorai. Ana kiran mai yin wannan zanen "Sakki". Akwai kuma zanen wuta wanda mata ke yi cikin gida. Wannan zanen wutar asalinsa ba namu ba ne, matan Hausawa sun aro shi daga Dakarkari, suka ara suka yafa ya zama al'ada gare su. An fi sanin wannan da suna zanen ƙorai. Bunza (2002) ya bayyana cewa ta hanyar zanen ake isar da wani saƙo da kuma rarrabewa kan yankin da wannan abin zane ya fito.

Ganin irin ƙima da darajar da ke ga zane a yau, yasa naga ya dace a ƙyallaro, a kuma zaƙulo shi, sa'annan a fito da daraja da martabarsa ga idon duniya, domin ƙara jinjinawa tunani da ilimi na Bahaushe a idon duniya. Kasancewar wannan ɓangare bai samu kulawa ta fuskar nazari yadda ya kamata ba, ya sa aka baza shi bisa faifai ga idon masu karatu da yan kallo don ɗaga martabarsa. Wannan maƙala za ta yi duba zuwa ga hikima da fasahar matan Hausawa ta zanen wuta a yankin Sakkwato.

## 2.0 Zanen wuta

Tun da muna maganar zanen wuta. Za mu so mu san ma'anarsa ta fuskar ra'ayoyin masana da kuma ta ɓangaren su Kan su mata masu aiwatar da shi, sa'annan mu bayyana kayan aiki da ake yin zane da kuma yadda ake yinsa.

## 2.1 Ma'anar Zaáneè

Ta fuskar ra'ayoyin masana da bayanan da aka samo daga ƙamusu, Kamusun Hausa (2006:489) ya bayyana ma'anar zane:

*Tana daga cikin ajin Suna. Ma'anarta shi ne sura ko layuka da aka rubuta a kan takarda ko rairayi ko wani bango ko kwali.*

Shi kuwa Kamusun Longman (2005:424) cewa ya yi:

*Hanya ce ta zana ko suranta wani da nufin ya zama wani abu ko kuma zanen ya haifar da wata sura.*

A fagen masu abu, da na tuntuɓi Malama Uwani mai sana'ar zane cewa ta yi:

*Wani azanci ne na yin rubutu ko zana sura da ake yi da wuta ga kayan aiki ko abin amfani ko na ƙawa domin ƙawatarwa da ƙarawa abin nan kyau da daraja da ɗaukar hankali da isar da saƙon magana ga mai kallo.*

Idan muka dubi waɗannan ma'anoni, sun bayyana muna zane dai wata hikima ce ba kowa aka bai wa ita ba, sai mai iya sarrafa abubuwa ga wani abu ko bagire domin ya bayar da wata ma'ana ko sura ko bayani ko ya zama kwalliya don ƙawa da ƙayatarwa. kenan dai zane na buƙatar mutum mai azanci da lissafi da saurin suranta abu a cikin tunani da sarrafawa a aikace.

Zanen wuta mata aka fi sani da shi, duk da cewa wasu lokuta maza suna sassaƙa kayayyakin aikin gida su hannuntawa mata, su kuma matan su shiga yin aikinsu na zanewa.

## 2.2 Kayan Aikin Zane

Akwai muhimman kayan aikin da ake tanada a lokacin da za a yin zane. Macen da take son yin zane dole ta tanade su. Da farko dai akwai wuta wadda ita ce uwar tafiya. Ana hura wuta, wasu ko sun fi yi da wutar murhu a yayin da aka ɗora abinci, ta kama ta yi garwashi. Sai tanaɗi nau'o'in duma da suka haɗa da dangin ƙwarya. Akwai wuƙar da ake karkare ƙwarya da ita. Sa'annan a tanadi tsinuka masu kama da tsinke, dogaye masu tsini, da wasu masu faɗi kamar guda uku ko huɗu. Sai ko magurjin da ake wasa tsinukan nan idan sun dallashe. Akwai kuma ƙyalle ko raggan da ake ɗaukar ƙarfe idan za a ciro shi daga cikin wuta, saboda yana yin zafi. Daga ƙarshe wacce za ta yi zane tana iya riƙe wata takarda ko sura a matsayin abin da za ta riƙa dubawa don  ta kwatanta shi da abin da take zanawa, idan har ba ta hardace abin da take son zanawa ba. Domin kuwa da yawan masu zane, idan sun ga abu, to sun riƙe shi cikin ƙwaƙwalwa, za su iya maimata makamancinsa. Su kuma masu koyo suna sha'awar aikin da yadda ake yinsa, yayin da masu saye abin yana ƙayatar da su ƙwarai, shi yasa suke sayen kayayyakin.

## 2.3 Yadda ake yin Zane

Bayan masu sarrafa duma ko itace sun gama nasu aikin, sai su gabatar da su ga masu aikin zane. Su kuwa matan sai sun sake goge abin da za a zanewa ta yadda zai bayar da sura mai kyau, ya yi sulɓi, sa'annan a hura wuta ta yi garwashi. Sai a ɗauko waɗancan tsinukan bayan an wasa su su yi kaifi, domin idan aka daɗe ana aiki da su dallashewa suke. A tura su cikin

wuta su ɗauki zafi. Sa’anan a riƙa jawo su ɗaya bayan ɗaya ana dannawa jikin ƙwarya ko wani abun da za a sarrafa. Nan take wutar za ta kama wurin da aka manna ƙarfen ta yi baƙi. sai a riƙa zanawa a faro daga sama zuwa ƙasa, har a cike abin da zanen. Idan ƙarfen da aka fitar da shi ya sha iska ko ya cire zafi, sai a mayar da shi cikin wuta a fito da wani mai zafi a ɗora inda aka tsaya har a ƙarasa. Sai dai ko ba a zane kayan ba ana amfani da su a ayyuka na yau da gobe. Zanen na ƙarawa kayan martaba ne kawai.

## 2.4 Kayan Aikin da ake Zanewa

Daga cikin kayan aikin gida na Bahaushe akwai waɗanda ake zanewa, kuma ko a zanen ya danganta. Wasu kayayyaki ba zanen wuta ake musu ba, kamar randunan da ake yi da laka ana sanya musu kala ne. wasu dangin duma kuma ana yi musu zanen aska ne. Su kuwa waɗannan za a kawo ƙasa, su ne ake yiwa zanen wuta kamar haka:

1. **Masaki:** Shi ne babbar ƙwarya wacce ake girke hura da ita, wasu lokuta ana yin kiɗa na buki da aka fi sani da kiɗan ƙwarya. Akan samu babban masaki a fara zanensa daga sama har zuwa ƙasa. Ga al’ada dangin gidan amarya ke aikawa dangin ango masakin kiɗa, kuma sai sun zaɓi mai ƙwari mai girma wanda ya isa. Wasu lokuta har jiƙa shi ake cikin ruwa ya yi kamar kwana biyu, don ya ƙara ƙarfi. Sai su aika da saƙon cewa idan an kashe shi saboda duka, a kai musu ɓalgace. Su ko gidan ango za su yi iya ƙoƙarinsu su yi kiɗan da za su fasa shi, sai a yi wasoson guntayensa a aika musu da shi. To yanzu akwai masu son zane masakinsu a yi masa zanen ƙawa da furanni ta fuskar rubuta kalamai na taya murna da rubuta sunan mata da miji ga masakin da hoton hannaye da rubutu, misali “gare ki mai babban damtse, lokacin abu a yi shi”.[1]


**Hoton Masaki**

[1] Hira da Hauwa Aliyu, ‘yar Akija Sokoto. Ranar 29/01/2015 da ƙarfe 2:00pm

2. **Kwarya:** su ne ƙananan ƙorai na aikin gida kamar wanke shinkafa da ɗibar ruwa da kuma mara ta ɗibar tuwo da kwacciyar mulmula tuwo. Girmansu ya danganta, domin ana samunsu bi da bi. Suna da matuƙar ƙayatarwa a wajen aiki musamman ga sabuwar amarya. Bayan aikin gida kuma ana jera su ga bango ta fuskar sagale su ga ƙusa, a manna su don ƙawa. Da yawan waɗannan su ma suna ɗauke da zanen abubuwa mabambanta na ƙayatarwa da sunan ango da amarya.


**Hoton Kwarya**

Bayan wannan akwai wata nau'in ƙwarya da ake tsagawa gida biyu, wato ɓare. Ita ko ba zanen wuta ake yu mata ba, ana sa tsinke a zane ta, ta fuskar fitowa da irin nau'in zane ko rubutun da ake so. i a nemo kaloli na fenti sai a shafe masa don ƙawa. Sa'annan a bi duk inda ba rubutu ko fenti sai a ƙwalbace ƙwaryar. Ita wannan ƙwalbatar ana yin ta da ƙaramar wuta. Ana ajiye ƙwaryar ɓare, wacce tana iya zama da gindinta saman teburin ma'aikata ko saman kanta da sauransu.[2]



**Kwaryar da aka ƙwalbace**

---

[2] Hira da Malama Yalwa gidan Haki. Ranar 29/12/2014 da ƙarfe 3:00pm

3. **Ludayi:** abin da ake amfani da shi wajen shan nau'in abinci mai ruwa-ruwa. Da duk aikin da ya shafi wannan abinci, kamar dama kunu da fura da sauransu. Ludayi ya kasu gida biyu, akwai ludayin ice akwai na duma. Dukkaninsu ana zane su. Shi ma kamar sauran takwarorinsa, ana zane shi tun daga kai har wutsiya. Sai dai su ba a cika yi musu rubutu ba, sai dai zane kaɗai.






**Ludayin Duma** **Ludayin icce**

4. **Maburkaki:** wani dogon itace da ake heƙewa, mai ɗan kauri, tsawonsa kamar zira'i. sai a sake yanko wasu karan itacen da ba su kai faɗin na farkon ba, a yi musu guntu-guntu ƙanana. Sai a ɗora saman kansa tare da taimakon siliya ko zare sai a ɗauresu tamau. Saman zai zama na murzawa da hannu bibbiyu, ƙasan zai zama na sakawa cikin abinci a yayin da ke markaɗe abu. Maburkaki ana amfani da shi wajen burkaka miya da nufun ta gutsuttsure ta yi laushi kar ta zamo tsage-tsage. Musamman idan aka sanya kabewa (kabushi), ba kasafai yake narkewa ba sai ya sha wuta mai yawa. To maburkaki na taimakawa wajen markaɗe kabewa, domin miya ta yi kauri. Masu tu'amali da nono ko ƙwame ko tsamiya da makamantansu, duk suna amfani da shi. Ana zane sirɗaɗensa da karan da ake gicciya masa.


**Hoton Maburkakai**

5. **Kujera:** itace ake sarrafawa a yi abin zama ta fuskar tsugunno. Kujera ana sassaƙarta ne daga itacen ƙirya ko nau'in itace masu ƙarfi. Kujera ta samu babbar martaba a gidan Bahaushe. Tun daga ɗakin dafa abinci da take taimakawa gaya a lokacin da ake aikin abinci don zama a sama, har zuwa ga tsakar gida a lokacin wasu ayyuka da zaman hira. Da kuma amfani da ita a bayi (banɗaki) da wasu ke yi don ta taimaka musu su zauna a lokacin da suke yin wanka, musamman matan da ke biƙi. ita ma ana zane ta daga samanta wajen mazauni kaɗai ba tare da ƙafafu ba. Amma mafi yawan zanenta ya fi karkata kan kara-kara ba sura ba.



**Hoton Kujeru**

6. **Turmi da taɓarya**: ana sassaƙa su daga itace. Turmi shi ake zuba abin da za a daka, ita kuwa taɓarya da ita ake dakan. Ita taɓarya ba a damu da yi mata zane ba. Shi kuwa turmi ana zane gaba ɗayansa. Akwai babban turmi na surfa da dakan abubuwa daban-daban. Shi wannan ba a zane shi, domin akasari za ka tarar tsakar gida ake barinsa ga gidan yawa. Shi kuwa wannan nau'in turmi ƙarami ne amare su suka fi sayensa domin yana da ban sha'awa. Ana zane duk bayansa. Da yawan waɗannan turamen ana yi musu murfi na itace wanda yake da abin riƙawa idan za a buɗe.[3]



**Hoton Turame**

[3] Hira da Tuni Muh'd, mai turame, Rungumi area, Sokoto. Ranar 06/09/2015. Karfe 5:00pm.

7. **Muciya:** itace ake sassaƙawa a feƙe shi a yi masa siffa mulmulalliya. Daga can samansa ana nuna alamar mariƙi. Babban amfanin muciya shi ne tuƙa tuwo da juya duk wani abu mai taɓo-taɓo kamar niƙaƙiyyar gyaɗa (labu) a lokacin da ake son ta fito da mai. Ko abu mai ruwa ko ruwa-ruwa kamar koko ko kunun zaƙi, idan an yi shi da yawa ana so a juya. Ita ma muciya ana yi mata zanen wuta tun daga farkonta har ƙarshe. Amma ita ma ba a cika yiwa muciyar da ake amfani ga abincin taro ba, sai marar yawa ko na amare.



**Hoton Muciya**

### 3.0 Karatun da ke Kunshe Cikin Zane-zanen Gargajiya

1. Sassan kalmomi/jimloli. Da yawan abubuwan da ake zanewa ana yi musu rubutu kamar sunayen mutanen da aka yi dominsu, misali ango da amarya. Da kalaman taya murna kamar "Congratulation" ko Gimbiya "Allah ba da zaman lafiya". Ko kuma su ƙunshi karin magana kamar "Gare ki mai babban damtse, lokacin abu a yi shi".



2. Alamomi: ana zana alamomi masu ishara ga wani keɓantaccen al'amari. Misali a lokacin siyasar farko wato NPN da PRP, ana zana alamar gida da masara, makulli da hasken wuta da sauransu. Ko kuma a zana tutar Nijeriya ko dawaki da maiki wanda yake alama ce ta tambarin Nijeriya (court of arm) ko hoton gidan sarki wanda yake nuni ga alamar daular usumaniyya da sauransu.



**Hoton Gidan Sarkin Musulmi**

3. Hotuna: wasu lokuta kuwa ana yin hotuna na fulawoyi masu ban sha'awa da hotunan wasu halittu kamar kifi da ƙadangare ko hannu ko tsuntsu da sauransu.





4. Jadawali (graphs): har wayau a cikin abin da zanen ya ƙunsa akwai wasu layuka nau'i-nau'i. wasu a tsaye za a yi ta jera su wasu kuwa a gilme, domin su bayar da wani samfuri na zane. Ya kasance an jere su bisa tsari, bai ɗaya, a yi ta tafiya da su har sai an kai ƙarshen ƙwarya yadda ba wata kafa da ba a zane ba.

5. Adana tarihi: wani abin ban sha’awa da ke ƙunshe a cikin zane, yana adana tarihi, domin kuwa zanen yana tafiya da yayin da ake yi na zamani. Misali lokutan siyasa ana rubuta kalamai ko alamomin jam’iyyu da zai nuna cewa ga lokacin da aka yi wannan zane. Kamar lokacin Sarkin Musulmi Macciɗo, an yi yayin “Sai Baba”. Lokacin gwamnatin Aliyu Magatakarda Wamakko ana rubuta “Sai Alu” da “Baba Oyoyo” ga kamfen ɗin Janar Buhari da sauransu da dama.[4]

6. Taswira Misali taswirar Nijeriya: akwai kuma hikima da suke tattare da ita ta zana taswira ta yankuna kamar taswirar Nijeriya da taswirar yankin Sokoto da sauransu da ake yi musamman ga ƙoran da ake ajiyewa a matsayin ƙawa a wuraren ma’aikatun gwamnati.

7. Fito da Al’adar Al’umma: wannan zane yana taka muhimmiyar rawa wajen fitowa da al’adun al’umma ga idon duniya. Da yawan waɗannan zanen ana bambance su daga inda suka fito. Misali ƙwaryar da aka zane a Zuru, yanayinta da ƙawar da ake yi mata ta sha bamban da ƙwaryar da aka yi a Sakkwato. Domin da yawan baƙi da suke kawo ziyara ƙasar Hausa suna sayensu su yi guzurinsu. Kuma ana ajiye su a wuraren adana kayan tarihi domin masu kai ziyara su gani. A lokutan bukukuwan baje koli, kowane yanki na ƙasar Hausa suna gabatar da nasu kayayyakin fasaha domin nuna hazaƙarsu da fito da al’adunsu a idon duniya.



Kwaryar Sakkwato



Kwaryar Zuru

8. Kawatarwa: ƙawa abu ne mai tasiri ga zuciya da idon mai kallo. Wannan nau’in zane yana da ban sha’awa da ɗaukar hankalin mai kallo, kuma sun zama abubuwan da ake amfani da su wajen ƙawata muhalli da gyara abin amfani da kuma nuna shi a idon duniya.

[4] Hira da Innon –Inno, shiyar Hungumawa, Sokoto ta arewa. Ranar 25/01/2015. Lokaci 11:00am

## 4.0 Kammalawa

Zane yana da matuƙar muhimmanci ga al'umma, domin kuwa yana bunƙasa tunanin mai yinsa, ta yadda kullum ƙwaƙwalwarsa tana tunanin yadda za ta sana'anta ko suranta abu wanda zai burge 'yan kallo da masu saye. Sa'annan ya samarwa masu yi aikin yi, na rage zaman banza da mutuwar zuciya, kuma ya samar da sana'a mai ɗaukar hankali wadda ake yi da ra'ayi da ɗebe kewa, da dogaro da kai. Su kuma masu sayarwa, zanen na zamewa ƙima ga abin da suke sayarwa ya kuma janyo hankalin mai saye.

Har wayau masu amfani da su suna ganin sha'awarsu da faranta musu rai a lokacin da suka yi arba da kyakkyawar surar, da ƙara cusa ƙaunar wannan kayan da aka zane ga mai su. Ta ɓangaren zanannun kayan kuwa, ba ƙaramar darajantawa da fito da martabar kayan aka yi ba a idon duniya da kuma fifita su bisa ga waɗanda ba a zane ba. Idan kuwa haka ne, muna iya cewa zane yana da amfani sosai ta kowace fuska aka kalle shi, da kuma ta kowace jiha aka yada shi. Idan kuwa hakan ne, shawararmu a nan ba ta fi baiwa masu yin sana'ar ƙwarin guiwa na riƙo da ita a matsayin abin yi da yake taskace al'adunmu, da kuma kira ga ɗaliban al'ada da su waiwayi wannan fasaha don taskace ta. Su kuwa al'umma su bayar da goyon baya wajen bunƙasa ta. Gwamnati ta kawo ɗauki don bunƙasa wannan al'ada da sana'a.

## 5.0 Manazarta


Fox, F.et.al (2005) *Longman Dictionary of Contemporary English*. Pearson Education Limited, England.

Gumi, A.G. (2007) 'Sana'ar Kwarya A Garin Gumi', B.A. Hausa, Usmanu Ɗanfodiyo University, Sokoto.